Made for minds.



# Koyi Jamusanci tare da DW

Gano harshe da al'adun kasar Jamus ta kwasa-kwasan harshen Jamusanci kyauta ta kan intanet daga Deutsche Welle (DW).

DW ta dade tana samar da kwasakwasan zamani daban-daban akan harshen Jamusanci sama da shekaru 60. Kwasa-kwasan da ake gabatar da su cikin harsuna biyu sun dace da masu koyo a matakin farko. Masu koyo a matakin sama kuma za su inganta kwarewarsu ta shirye shirye na musamman, kamar telenovela na ainihi. Shin ka fi son karanta rubutu ne, saurarar faifan sautin murya, ko kallon hoton bidiyo, akwai abin da aka tanada ga kowane mai koyo. Ga wadanda kuma ke son yin amfani da kwasakwasan amma ba ta kan intanet ba, to za a iya sauko da abubuwan karatun.

dw.com/learngerman/hausa

## Audiotrainer
## Darussa 100 don sanin kalmomi




A1 A2 B1 B2 C1 C2

**Harsuna**
Harshen Chaina, Ingilishi, Faransanci, Portuguese, Rashanci da Sifaniyanci

**Kayan karatu**
Takardun aiki da littafin aiki (za a iya saye daga www.book2.de)

Za ka iya sanin kalmomi da **Audiotrainer** don taimaka maka ka san muhimman abubuwa sannan kuma ka inganta yadda ka ke furta wa. Akwai darussa 100 wadanda za su taimake ka koyon yadda za ka yi tambaya sannan ka sami natsuwa a cikin rayuwar yau da kullum a Jamus. Duk kwasa-kwasan za a iya amfani da su akan intanet ko kuma a sauke a sigar fayil na MP3, ko kuma kana iya yin rijista da gaba dayan yankunan karatun ta podcast. Audiotrainer zai ba ka damar koyo a yanayin saurinka.

**dw.com/learngerman/hausa/audiotrainer**

## Deutsch – warum nicht?
## Kwas din harshen a sautin murya na gargajiya




A1 A2 B1 B2 C1 C2

**Harsuna**
Jamusanci, Ingilishi da wasu harsuna 26

**Kayan karatu**
Takardu da littafin darasi da za a fitar a takarda

**Deutsch – warum nicht?** Yana ba da labarin Andreas a kashi hudu – dalibi da ke aikin tsaron kofa a otal.
Kowane kashi yana samar da darussa 26 da za a iya saukewa wadanda suka hada da hirarraki, bayanai akan nahawu, ayyuka, da kuma fayiloli na sautin murya. Kwas din da harsuna biyu ake yinsa, don ka iya koyon Jamusanci a natse cikin harshen da ka fi sani. Ana samunsa cikin harsuna daban daban har guda 28.

**dw.com/learngerman/hausa/warumnicht**

## Deutsch Interaktiv
## Kwas din koyi-da-kanka na kan intanet




A1 A2 B1 B2 C1 C2

**Harsuna**
Jamusanci, Ingilishi, Rashanci

**Kayan karatu**
Ayyukan cudanya, kamus, taimakon nahawu, takardun aiki da kuma jan hankali kan nazari

**Deutsch Interaktiv** na samar da ayyuka masu dama, fayilolin sautin murya, faya fayen bidiyo, da kuma jerin hotuna don kara armashi ga koyo. Gundarin bayanin nahawu da kuma kamus mai sama da kalmomi 7,000 da nuna yadda ake furta su kan saukaka koyo. Yi rijista kyauta don ka bude shafinka na koyo. Shirin ka adana sakamakonka kuma ya yi maka jagora a cikin kwas din. Ta haka, zaka iya tsara lokacin koyo ya dace da muradunka.

**dw.com/learngerman/deutschinteraktiv**

## Jojo sucht das Glück
## telenovela don koyon Jamusanci




A1 A2 B1 B2 C1 C2

**Harsuna**
Jamusanci

**Kayan karatu**
Ayyukan cudanya, takardu da taimakon kalmomi, takardun aiki da bayanin darasi don malamai, takardun bango da kuma sautukan kira

Koyi Jamusanci ta wata fuskar daban tare da **Jojo sucht das Glück**. Marhaloli uku, kowacce dauke da darussa 33 da kuma ayyukan cudanya, zai taimaka maka ka inganta kwarewarka akan harshe a cikin sassaukar hanya mai nishadi. Da wa zai yi zaton cewa Jamusanci zai iya kasancewa harshen soyayya?
Kasance tare da Jojo daga Brazil a fafutikar da ta ke don samun farin ciki, rayuwa da kuma soyayya a sabon garin da ta ke zaune, wato Cologne!

**dw.com/jojo**




Available on the App Store

ANDROID APP ON Google play

Deutsche Welle | DW Akademie
Bildungsprogramme
53110 Bonn | Germany

bildung@dw.com
© Deutsche Welle 2015

dw.com/deutschlernen